ture hannun nasa tayi ta kuma tashi zata bar masa gadon yayi saurin janyo ta zuwa jikinsa yana rarrashi cikin son yi mata bayanin yanda sukayi da umma,da sauri tasa hannuwanta duka biyu ta rufe kunnuwanta ita bata son jin komai daga gare shi tunda har ya mata gami da umma.
Bai fasa rarrashin ta ba cikin kalaman nn nasa masu dad'i da tausasa zuciya har ya samu yayi nasarar janye hannuwanta da ta rufe kunnuwanta yana fad'in"haba my lady na am sorry kinji bazan qara miki irin haka ba kuma albishirin ki"
A shagw6e cikin kuka ta maqale kafad'a ita bata son ji.
Yace"umma fa ta amince na samar miki admission a school d'inda su zeenah ke karatu"
Sake maqale kafad'a tayi tana kallon sa ita bata yarda da zancen sa ba wasa yake mata.
Yace"Allah my lady da gaske nake gaya miki na bata haquri ta kuma amince amma da sharad'in duk kika yi wani abinda ba dai dai ba in gaya mata shike nn sae a cire ki daga karatun gabad'aya ko wata makarantar ma baza a nema miki ba sae dai kiyi ta zama a gida kina kallo su zeenah naci gaba da karatu abinsu"
Bintu dake kallon sa idanun ta cike da qwallah tace"inshaa Allah yaya nayi alqawari bazan yi wani abinda ba dai dai ba"
D'auke da murmushi yasa hannun sa ya share mata hawaye yana fad'in "yauwa to shike nn yi shiru daina kuka"
Nan taje a hnkli kan faffad'an qirjinsa ta lafe abinta tana sauraren yanda yake shafar gadon bayan ta a hnkli cikin natsuwa kmr wata er baby.

*_1 month later_*
Tuni bintu ta fara zuwa school sae jin take yanzu gabad'aya bata da wata matsala a rayuwarta, dama babban burinta shine tayi karatu kuma gashi Allah ya taimake ta ta fara abinda bata ta6a zato ba.

Tafe suke ita da su sarah sun rako ta zasu fito gate d'in uduth sae rarraba ido bintu keyi ko zata hango motar waheed tafe.
Zeenah dake kallonta ta le6ace baki snn tace"hm dama kin daina wani dube dube dan ga dukkan alama waheed ya manta dake"
Sarah tace"lallai dae kam ace tun d'azu da kuka gama lectures kin kirasa ya turo miki driver amma har yanzu shiru munyi zaman jira har gamu zamu fito gate ba alamar motar shi tafe gashi ba ko gida zaki je ba bare ki taka a qafa.
Bintu tace"shi ne wlh amma bana tunanin yaya waheed ya manta da akwai dai abinda ya tsaida drivern.
Zeenah tace"hm haka dai kk gani wata qil ko kiran sa ma baiyi ba yana can yana harkokin gabansa da suka fi masa muhimmanci.
Kafin bintu tace komai sae ga motar waheed ta faka a gaban su wato drivan nata yazo

d'aukar ta,da saurin sa ya sauke glass yana fad'in"dan Allah hjy ayi haquri wlh go slow ne ya tsaida ni.
Bintu tace ba komai snn ta kalli zeenah tace"inace yanzu kin tabbatar nafi komai muhammanci a gurin yaya waheed kuma ba manta ni yayi ba ehe.
Ta qarashe mgnr ne had'e da mata gwalo ta kuma yi saurin bud'e mota ta shige sae dariya take sbd dukan da zeenah taje kaimata bata same ta ba.
Ta rufe ganbun mota snn tayi ma sarah hannu tana fad'in"Bye Sarah keda kk da d'an hnkli hnkli ke kad'ai zanyiwa bye bye.
Da sarah har zeenah dariya sukayi had'e da yi mata bye bye har motar su ta fita snn suka kama hanyar komawa hostel zeenah ta qyalqyace da dariya tana kallon sarah snn tace"sarah mae d'an hnkli hnkli"
Sarah tace"uhm barta abin tausayi sae nn gaba zata gane ainihin sarah.

A 6angaren bintu kuwa suna fitowo gate ta snr da driver gidan antin ta Hafsa zai kaita.
Da yake anguwar ba wani nisa,
take suka isa.

Yana kaita ya juya bae jirata ba kmr yanda ta buqata.
Tana shiga harabar gidan ta had'u da twins en qananun yara maza su biyu suna ball.
Suna ganin ta suka zo da gudu.
Anti oyoyo!anti oyoyo!
Cike da murna Bintu ta d'auke su tana fad'in"yeeh Abba da daddy kuna lfy ina maman ku"
D'ayan yace"mama aya ciki aya kayyo"
Bintu ta fashe da dariya tana fad'in"hehehe lallai anti shine tace min kun iya magana narai narai har ma zaku iya saida mutum ashe yamin baki ma kuke.....Aa bazan daukar miki ba kar ki ma 'ya'yana sharri.
Cewar wata kyakkyawar mata da ta fito er sililiya fara tas hanci har baka kmr bafillata duk dae kmr su d'aya da bintu dan kallo d'aya zaka musu kasan en uwan juna ne.
Bintu tace"ba wani sharri anti ai kinsan gaskiya na fad'a ina 'yata ilham?
Hm er ki mae halinki da qyar yau in gaya miki na samu taje islamiya wae tunda taji zaki zo ita bazata ba Abbanta yaja ta suka tafi sae kuka take.
Bintu tace"Allah sarki ilham ae zata dawo ta sameni ina nn sae bayan isha'i"
Uhm iyayen rigima ae saida na gaya mata hk amma taqi yarda,sorry zo mu shiga daga ciki na barki tsaye.
Ae na d'auka ko wani abu ya fito dake anti.
Inafa muryar ki na jiyo kina ma 'ya'yana sharri shine na fito.
Uhm wae anti kina fad'in na musu sharri bayan ga gsky nn a bayyane basu iya magana ba sae yamin baki sun kasa iya magana har yanzu.
Bintu ta qarashe mgnr ne had'e da zama kan kujera dan koda take mgnr sun shigo daga ciki ta sauke yara suka koma abinsu waje suka ci gaba da ball.
Anti Hafsa ta kawo mata lemu da ruwa had'e da abinci ta zauna tana fad'in"Bintu er boko shike nan kin mana wayo kin fara school abinki sae naji kmr nice wlh amma ina karatu ya min fintinkau"

Bintu tace"kan me zaki ce hk Anti hafsa ae ko yanzu bata 6aci ba kina iya kiyi karatun ki meye matsala ko ganin kk yara baxa su barki ba"

Hm Bintu ae in ta yara ne ma da sauqi Abban ilham ne bazai barni ba,ba irin roqon da ban masa ba kan nima ya barni inyi karatu nn wlh ya bushe ido yace ba wani karatu da zanyi,nayi kuka har nagode Allah ke har kukan ma yaja min zazz6i amma mutumin nn yaqi tausaya min.

Bintu tace"cabd'i yanzu anti duk irin qaunar da yaya Yusuf ke maki amma yaqi ya barki bayan yaji labarin Abba yace ya yarda muyi karatu idan sun bar mu.

Hm bari kawai ae yaya Yusuf d'in ne da kishi kinsan fa tunda akayi auren mu baya bari in fita koina sae da niqab.

Bintu tace "to Allah kyauta,Haka itama Anti Nafee da naje gidan ta kwanaki ta gaya min da qyar ne ko yaya sadiq zae barta dan taga ko mgnr karatun ma baya son ta mishi,nace taci gaba da lalla6a shi ko Allah zae sa tayi nasara.

Anti Hafsa tace" to Allah yasa ta dace d'in"

Bintu tace"Amin"

Wacce sae a snn ne ta fara cin abinci byn ta gama suka tsiri wata firar.

Nan bintu ta yini har bayan isha'i snn ta soma shirin komawa gida.

Zaune suke kan bed Anti Hafsa ta bata kayan mata tana mata bayanin yanda zatayi amfani dasu.

Bintu tace"Anti Hafsa da kin barsu"

Anti Hafsa tace"meyasa?

Er dariya bintu tayi snn tace" Hm bari kawai kedai Anti kwanaki da kika bani wasu na gwada hahaha daren rnr na darzu a gun yaya waheed in gaya miki wlh har saida na masa kuka snn ya barni hkn bae hana da safe ya sake nema na ba,hm ni na rasa wane irin mutum ne shi da sam baya gajiya da wnn harakar.

Anti Hafsa tace"ba dole ba ya had'u da er shila"

Hm anti knn ko ba hk ba kinsan fa na cika cin dabino,kwakwa,rake,jiqaqqar aya,mazanqwaila,duk gabad'aya nabi na maida su qwalamata,har shi kanshi yaya waheed na koya masa cinsu da kullum in ya fita sae ya siyo mana, gashi bini bini duk sae nayi mana kunun aya kuma duk dare kafin mu kwanta idan bana sha madarar pick ta ruwa ba bana jin dad'i.

Anti Hafsa dake sauraren ta tayi dariya snn tace"kice ke kika sa waheed ya iya jaraba"

Uhm wlh kuwa anti kullum idan ba ya neme ni ba baya jin dad'i har ma ya saba min da halin shi dan wata ran da kaina sae in neme shi mu kashe juna da soyayya.

Ta qarashe mgnr ne cikin dariya.

Anti Hafsa ta girgiza kae tace"oh bintu ba kunya"

wace kunyar kuma anti mijina ne fa abun qaunata da mukayi auren so bana qiyaya ba.

Murmushi kawai anti Hafsa tayi had'e da girgiza kanta snn tace"nidai gaya min still d'in baza ki tafi da kayan ba ko kuwa?

Bintu ta kar6i kayan ta jawo bedside drawer ta maida tana fad'in"ki barsu kawai anti dan wa en can ma da kk ban suna nn basu ko qare ba"

Nan ta hango wani abu a cikin bedside drawer d'in tasa hannu ta d'auko snn tace"Anti wnn abun fa ya ake amfani dashi gaya min ina so ya ban shawa"

Da sauri anti Hafsa ta kar6e tana fad'in "iya kanki wlh wnn na manyan mata ne ba irinku da ko

haifuwa bakuyi ba"
Bintu ta shgwa6e fuska tana kallonta kafin tace komai anti hafsa taja hannun ta tace"tashi muje in rakaki ga drivern ki can yazo sae oda ake tayi.
Bintu ta tashi ta d'auki mayafinta da jakarta tasa takalmi tana fad'in "yau anti korata ma kike"
Na isa ba korar ki nake ba rigima dai naga zaki zo min da ita.
Bintu tayi murmushi dai dai sun iso falo tace"ilham, daddy Abba, yaya Yusuf ni zan tafi sae kuma wani lokaci idan na koma shigowa.
Ilham tazo da gudu ta riqa hannun bintu.
Yaya Yusuf ya riqo hannun Abba da daddy suka fito su duka har anti Hafsa suka rakota har gate ta shiga mota ilham sae bye bye take mata bintu na mayar mata har motar su ta wuce snn suka juya suka koma daga ciki.

Bintu na isa gida kae tsaye d'akin waheed ta nufa ta tura qofar d'akin a hnkli cikin sallama wani irin sanyin dad'i da dadd'an qamshi ya d'aki hancinta ga d'akin luf luf ba wani haske sosai,ta shiga ta maida qofa ta rufe
sae ga waheed ya fito daga bathroom gurin wanka zir d'insa ba komai a jikinsa daga shi sae d'an qaramin towel a hannun sa yana goge gashin kansa.
Yana ganin ta ya ware mata hannayen sa cike da murmushi,
ta qaroso ya rugunmeta yana fad'in"oyoyo my lady kin dawo"
Bata ce masa komai ba sae shagwa6e masa fuska da tayi.
Ya riqa hannunta suka tafi kan bedside suka zauna,ya d'aura tafin hannun sa a hnkli kan gefen fuskarta yana kallonta da kulawa snn yace"mene wa ya ta6a min ke gaya min kinji"
Bintu dake kallon sa a shagwa6e takai hannu kan faffad'an qirjinsa ta tafi dashi a hnkli har izuwa kan tsakiyar cinyoyin sa ta kama abinda yafi matuqar so ta ta6a a jikinsa ta shiga shafa gurin a hnkli cikin qara shagwa6e fuska tana kallon sa snn tace"ba kae bane kaqi zuwa ka d'auko ni sae driver da ka tura min"
Waheed dake kallonta ya lumshe ido cikin jin dad'in shafar shi da take ya kwantar da muryar sa sosai yana"fad'in"am very sorry my lady yau a gajiye na dawo shiyasa amma da kaina naso inje in d'auko ki"
Tace"To me yasa kayi wanka baka jira na dawo muyi tare ba?
Sae da yakai babban yatsan sa kan d'an qaramin bakin ta da ta turo ya shafi lips d'in ta a hnkli snn yace"sorry once again duk gajiyar ce ta kawo min hk amma muje in miki wankan da kaina koh"
Murmushi bintu tayi tana kallon sa cike da so yasa hannu ya soma cire mata kayan jikinta har ya cire mata komai ya d'auke ta ya d'aura kan cinyoyin sa sae kallon nonuwanta yake da kulawa, yakai hannun sa kmr da tsoro yana shafa su snn ya kalli bintu yace"Fatima kaddai wani abu kk shafawa a nonuwan ki dibi yanda suka qara cikowa"
Bintu ta kalli nonuwanta d'auke da murmushi dan jin zancen nasa tayi da kamar zolaya.
Ta d'ago ta masa wani d'an kyakkyawan kallo snn tace"uhm yaya knn ka kuwa kalli anti babba kafin ka kalli qirjina"
Da rashin fhmta waheed yakai duban sa a tsakiyar cinyoyin sa ya kalle ta yace" fatima mene ne ni banga wani abu ba"
Tace"baka ga irin girman da anti babba ta qara ba?

Da saurin sa ya koma kallon tsakiyar cinyoyin sa hannun sa akai sae dubawa yake amma baiga wani qarin girma ba,
ya d'ago yana mata kallon tuhuma dan ya fahimci zolayar sa kawai take,
Cikin dariya bintu ta tashi zata bar gurin ya kamota suka fad'i kwance kan bed yana kan jikinta ya kama kunnen ta yana dariya yace"kin raina ni koh?
Er qara ta saki tace"wash Allah yaya to ae kaine ka fara danni banga wani cikowa da mammana suka qara yi ba"
Ta qarashe mgnr cikin turo baki waheed yakai hannu zae matse bakin tayi saurin saka tafukan hannayen ta ta rufe fuskarta ya shiga yi mata cakulkuli bata bud'e fuskar ta ba sae zille zille take tana dariya tana fad'in yayi haquri.
Waheed ya tsaya cak da mata cakulkuli yana kallonta a kasale da idanun sa dasu ka soma canza kala.
Nan bintu ta bud'e fuskarta a hnkli tana kallon shi d'auke da murmushi tace"yi haquri yaya bazan sake ba.......kan ta qarasa sae jin bakin sa tayi a nata ya cafki harshen ta ya soma tsotsa tamkar ya sami wani hadadden sweet,idanun sa a lumshe sae shafa jikinta yake ta koina tana ji har da wani 6ari jikinsa keyi.
sha'awar gogan nata ta gama kae qololuwar motsa masa knn ae kuwa sae ta bashi kae bori ya hau dan itama tun shigowar ta d'akin ya fara tada mata tata sha'awar.
[12/6, 6:27 AM] Billygiro😊: *_🎱BINTUWAHEED🎱_*

*_Story n written by Billy giro😊_*

*_page 7_*
Washe gari da asuba koda waheed ya tashi baiga bintu ba ya tashi sae miqa yake had'e da salatin annabi dake fita bakin shi.
A tunanin sa bintu tana bathroom amma koda yaje bata ciki yayi brush had'e da arwala snn ya fito,ya nemi farar jallabiyar sa ya saka.
Bintu kuwa na kitchen tana d'aura danbun shinkafa er gote da aka 6arje dan haka kawai tunda kirayen kirayen sallah ya farkadda ita taji ba abinda take so irin taci danbu.
Waheed ne ya shigo kitchen d'in yayi tsaye a bakin qofa hannuwan sa a hard'e kan qirjinsa sae kallonta kawai yake.
Qamshin turaren sa ne ya fahimtar da ita yana gurin ta d'ago ta kalle sa d'auke da murmushi tace"sannu yaya ka tashi"
D'an guntun murmushi ya sakar mata ya qaraso gurinta hannun sa kan qugunta ya d'an tafi da ita zuwa jikinsa yana kallon abunda take yace"fatima me kike d'aurawa tunda asussuba haka ko

sllh ba'ayi ba?
Wlh yaya haka kawai ina farkawa naji ba abinda nake son ci irin danbu.
To ae da kin bari anyi sllh tukun koh,
Yaya bakaji yanda nake jin son sa a raina bane kuma gani nayi tunda ina da komai na had'in shi gashi kuma ina shiga school gwanda inyi in kammala in samu in d'aura maka naka break fast kafin lokaci ya tafi.
Aa ae ba sae kimmin nawa break fast ba muci danbun naki kawai dmn bana son ki wahala da yawa.
Murmushi bintu tayi dae dai ta kammala had'a danbu ta zuba suka fito waheed ya nufi masallaci ita kuma taje d'aki tayi arwalla tayi sallah.

By 7am tuni danbun ta ya nina dan harma sunyi wanka sun shirya snn suka tafi kan dining bintu ta zuba musu a plate d'aya kmr yanda suka saba,ga kunnun ayan su a gefe cikin jug yayi sanyi har ya gaji,suna ci sae santi waheed keyi kan irin yanda danbun yayi matuqar taushi da dad'i kyace kuskus, in kuma yasha kunun aya har da wani ajiyar zuciya yake yi bintu dae sae dariya take in da sabo ta saba dan dik tayi girki sae yayi ta santi yana yaba girkin kyace rnr ne ya fara cin girkinta.

Bayan sun kammala cin abincin ne guraren 8am suka fita ya ajiye ta school snn ya wuce gurin aiki,dama haka sukeyi kullum shi ke kaita school idan ta gama lectures ta kirashi ya turo mata driver ya maida ta.

Bayan kwana biyu da faruwar haka waheed ne a gidan wani abokin sa da suke matuqar shiri.
Abinci suke ci suna fira waheed yace"ni kuwa Khalid sae naga kmr fushi kake da Zainab "
Khalid dake kallon sa yace"me ka gani?
Gani nayi da ka kirata mu gaisa  har ta kawo mana abinci sae wani fusfuskewa kake kana faman shan toka ko kallon ta baka sonyi sae ma danne danne da kake a wayar ka har ta qaraci jera mana abinci ta wuce ba ko sannu da aiki sae ni kad'ai da na mata sannu.
Khalid yace"waheed knn to so kake in sake mata fuska ta samu damar raina ni"
Da mamaki waheed yace"as how Khalid matar ka ce fa da kukayi auren so bana qiyayya ba idan bata ji dad'i a gurinka ba a gurin wa zata ji to"
Waheed kasan fa bana son raini ko kad'an mace kuma tana da wani abu da zarar taga kana sake mata fuska kuna wasa da dariya sae duk tabi ta rainaka,shiyasa har kullum mamakin ka nake da ka auri wnn er qaramar yarinya da bata wuce ka raina ba wacce na tabbatar in banda sagar ci da rainin wayo ba abinda take maka a cikin gidan.
Waheed yace"Khalid zancen ka yasa nayi matuqar jin kunya dmn duk a tunani na kasan abinda kakeyi sae naga ashe baka sani ba.
Mace fa da kake gani itace uwar mu abokiyar rayuwar mu itace jin dad'in mu,itace komai namu idan babu mace tofa har da mu mazan babu.
Kan me to zaka nemi ka takurawa mace akan kawai kar ta rainaka anya kuwa khalid kayi aure ne dmn koyi da  manzan Rahama......kaga waheed dakata ba wa'azi nace kamin ba kuma ina so ka fahimci cewa daa da yanzu ba d'aya bane haka matan daa da na yanzu baza su ta6a zama d'aya ba,kuma ni ra'ayina ne bazan iya sakewa mace ba in bata damar raina ni shiyasa

kaga na auri wacce ta girma tasan kanta ba qaramar yarinya ba.
Er dariya waheed yayi snn yace"Khalid knn dani da na auri qaramar yarinya da kai da ka auri wacce tasan kanta duk a masu aure za'a kiramu asalima nafika jin dad'in rayuwar auren nida na sake da matata muna wasa da dariya cikin jin dad'i babu wani takurawa juna da muke.
Amma kai kanka ka takura kanka da kanka bama ita kad'ai ba tunda in ka shigo cikin gida babu wani sauran sakewa kana nn shaye da toka har sae kuma ka fita.
Wae ma tukuna in tambaye ka cikin baka son rainin ne kake had'a gado d'aya da ita har ta kae ga ka qunsa mata ciki har gashi nn ya fito kowa na gani a bayyane,nikam wace irin rayuwar aure ce kukeyi wnn Khalid yama kuke mu'amalar kwanciyar auren naku to a shaye da tokar ne kake yin komai, tell me kayi shiru sae kallo na kake.
Jiki sanyaye Khalid yace"is ok waheed naji nayi kuskure zan gyara.
Da yafi maka dan zaka fi jin dad'in rayuwar auren, kuma Allah yasa da gaske zaka gyara d'in ba fad'a kawai kayi ba dan ka huta dani dan nasan halinki ba yau ba.
Er dariya Khalid yayi yace"Allah dagaske nake gaya maka waheed fatana Allah ya bani ikon gyarawa kmr yanda nayi niyya.
Waheed yace"Amin"
snn ya tashi a cewar zae tafi ya bar ladyn shi ita kad'ai a gida.
Khalid yayi dariya yace to muje in raka ka mota ka tafi kar ta gaji da zama ita kad'ai agida ta ajiye kuka.
Waheed yace"kaga kuwa ba zan so kukan ta ba gwanda in gaggauta komawa in ga er leleta.
Murmushi kawai Khalid yayi yana mae qara jin qarfin gyara rayuwar auren sa da zainab dan sae yaji duk waheed ya birge sa.

Koda waheed ya dawo gida kae tsaye d'akin bintu ya nufa ya same ta zaune kan dressing mirror d'aure da towel tana shafa mae.
Yaje ta bayanta ya rungume ta ta mishi sannu da dawowa bae amsa ba sae yaye mata towel yayi yana kallon nonuwanta,bintu ta d'an shagwa6e fuska dan a tunanin ta ko zae sake neman ta ne gashi kafin ya fita sae da ya neme ta,shine bata ko samu tayi wanka ba sae yanzu sbd baccin da tayi.
Waheed dake kallon nonuwanta yace"ni kuwa fatima wai har yanzu baki kula da mamman ki sun qara cikowa ba jifa"
Saurin rufe qirjin nata tayi da towel cikin shan toka irin ta shagwa6a tana mae doddoka qafafunta qasa tace"ni yaya ka daina min sa ido bana so"
Da surin sa ya kama kunnen sa yace"afwan na daina tunda ba kya so amma d'anyi min murmushi,ta maqale kafad'a baza tayi ba ya shiga tsokanar ta kama dariya.

Bayan wani d'an lokaci, rayuwar su na nn yanda suke yinta abun sha'awa kullum cikin nuna so da qaunar juna suke da wuya kaga fad'an su sae dai rigimar bintu wacce tuni waheed ya saba da ita,haka fannin kwanciya
sam waheed bayada baqin ciki dan in zai neme ta sau nawa a rana bazata hana shi ba shiyasa yake qara jin sonta a ransa.

Su zeenah kuwa suna nn kan bakar su na ganin cewa sun lallata rayuwar auren su kota halin qaqa.
 Bintu dae bata san komai akan nufin su ba sae karatun ta da tasa a gaba asalima kan irin shirin da suke bata ta6a kawo cewa zasu iya cutar da ita ba ko makamancin haka,shiyasa duk maganganun da suke mata idan sun had'u na ganin sun 6ata waheed akanta ta d'auka wasa ce kaiwa bata san cewa har cikin ransu abun yake ba dan bintu yarinya ce wacce in ta yarda da mutum to ta yarda da shine har cikin ranta.

Yau ta kasance weekend ne dukkan su suna gida ita da waheed suna zaune a garden suna shan iska ga garin yayi luf luf hadari ya kankama sae iska mae dad'i keta kad'awa duk inda farin cikin bintu yake ya tattaru guri d'aya dan a rayuwar ta tana bala'in son ayi ruwan sama ta shiga tayi wanka.
  Waheed kam gwanin tsoron ruwan sama ne sam baya son su duke sa shiyasa yana ganin an soma yayyafi yaja bintu suka koma ciki sae kukan shagwa6a take ta mai ita ya barta ta fito tayi wanka,yaqi ya barta dan baya son ta shiga ruwa zazza6i ya kamata.
   Ruwan na fara qarfi ta kyakyaci idanun sa ta lalla6a ta bud'e qofa ta fito aguje sae murna take tana tsalle tana rawa ga ruwan sae qara qarfi suke tasa hannu ta cire ribbon d'in kanta ta jefar sae tsalle take tana wasa da gashin kanta.
  Ba yanda waheed ya iya yayi tsaye kawai a bakin qofa  fuskar sa d'auke da murmushi yana kallonta tana ta wasa abunta cikin ruwa.
 Da ta hango shi tace yazo suyi wankan ya maqale kafad'a shi bazai je ba.
 Tayi dariya kawai taci gaba tsalle tsallen ta tana wasa da gashin kanta,
waheed dake kallonta sae duk ta bashi sha'awa ya ciro wayar sa ya soma video d'in ta.
[12/6, 6:27 AM] Billygiro😊: *_🎱BINTUWAHEED🎱_*

*_Story n written by Billy giro😊_*

*_page 8_*
 I Luv u ina sonka yaya!
 Bintu ta fad'i hk tare da jefo masa kiss dan ta fhmci d'aukar ta yake,
 shima ya mayar mata yace"I Luv u too my lady nima ina sonki"
Ta kirasa da hannu  kazo muyi wanka to.
  Ya girgiza kansa ba zai je ba tayi dariya sbd tasan ba zai zo ba d'in ta fad'a ne kawai.
  Cike da jin dad'i taci gaba da yin wankan ta shi kuma yana ta d'aukar ta har sae da ta gaji  dan

kanta snn tazo ta same shi nn inda yake tsaye a bakin qofa zata cire kayan jikinta dake ta faman tsiyayar ruwa waheed ya saka wayar sa a aljihu ya kama hannunta yace"Aa muje daga ciki"
A d'an shagwa6e tace"Uhm yaya ni bana son in jiqa gidan aikin goge goge ya sameni.
D'aukar ta yayi cak had'e da fad'in muje ni zan goge dan baxan bar wani ya ganki ya shamma ce ni ba.
Tace"kae yaya ae naga ba kowa a gidan sae mu kad'ai"
Yace"shi mae gadi fa ba mutum bane"
Mai gadi da yana can cikin d'akin sa ya zai yi ya ganni.
Aa nidai hankalina zae fi kwanciya idan muka shigo ciki.
To ae gashi nn duk ka jiqa kayan ka,
Yace"ba komai nidae burina in kare mutunci ki"
Cikin jin dad'in mgnr sa ta kai bakinta gefen fuskar sa ta masa kiss snn tace"nagode da qaunar ka a kaina.
Waheed yayi murmushi dai dai sun iso bathroom ya sauke ta,ta cire kayan jikinta shima ya cire nashi ta kar6a ta had'a da nata ta saka a washing machine snn sukayi wanka da ruwa masu zafi.

Da dare Bintu ce narke kan jikin waheed sae zuba masa shagwa6a take da ya rasa gane kanta.
Yace"wai ni Fatima gaya min me kike so"
Yaya ni bana son  in gaya maka kace a'a,
Bazan ce a'a ba gaya min.

So nake dan Allah muje kebbi ending of dis week wlh nayi kewar su umma sosai.
Da saurin sa ya tashi had'e da fad'in"may God bless u!ae kin tuna min gobe zanje kebbi kan wani d'aurin auren wani abokin mu da za'ayi ba kuma zan dawo ba sae Monday da yamma sbd wani meeting da zamuyi a can garin"
Bintu ta kama hannuwan sa cikin begin tace"dan Allah yaya kar kaje kace musu baza ka sami zuwa ba in yaso wani sati sae mu tafi tare dai dai mun gama test6 d'in da muke kaji"
Er dariya waheed yayi snn yace"to ae bazai yiyu bane Fatima,d'aurin auren zan fasa ko kuma meeting"
"Ka fasa kowanne in yaso sae ka basu haquri akan rashin samun zuwanka"
Ta masa mgnr ne cikin marairaice fuska.
Yace"hkn bazai yiyu ba Fatima dole ne inje, ba dan ma tests d'inda zakuyi ba ae da ke ya kamata ace naje"
Um um ni ban ma son kwana d'aya nafi son nayi kwanaki.
To kiyi haquri ki barni inje byn na dawo sae kuma muje a qarshen satin nn kmr yanda kk ce koh"
Uhm ni yaya bana son ka tafi ka barni nafi son in zaka je muje tare kasan bazan iya kwana gidan nn ni kad'ai ba wlh.
Kar ki damu ae gun mami zan kaiki cewa da mahaifiyar sa.
D'an guntun murmushi tayi tace"to shike nn ba komai amma....sae kuma tayi shiru bata ce komai ba.

Waheed dake kallonta da kulawa yace"amma me gaya min kinji
Cikin muryar kuka Tace"um um ba komai kawai banso ace zaka kwana ba kewar ka zata min yawa"
Sae da ya janyo ta zuwa faffad'an qirjinsa ya kwantar ya shiga shafa gadon bayanta a hnkli snn cikin muryar rarrashi yace"am sorry my lady ni kaina kinsan zanyi kewar ki ba kad'an ba, dan ba yanda zanyi ne amma nafison duk inda zanje ina tare dake"
Tace"Ni ina tsoro kar daga kwana d'aya kaje kafi haka"
Um um inshaa Allah kwana d'aya kacal zanyi in dawo kinji.
Kae ta gyad'a masa snn ta qara shigewa jikinsa ta lafe sosai kmr wacce akace za'a qwace ta daga gare shi.
Washe gari byn ya kaita gun mamin shi da zae tafi suka rako shi suna masa Allah kiyaye hanya bintu kmr tayi kuka dan idanun ta cike suke tap da qwallah waheed ya musu bye bye yaja motar sa da sauri ya tafi dan ya fahimci kuka bintu ke son mishi shi kuma ba son ganin kukan nata yake ba.

Ranar Monday mami da kanta ta d'auki mota ta kai bintu school da kuma suka gama abinda suke taje ta d'auko ta.
Su zeenah basu yi wani mamaki ba sbd sun san irin so da qaunar da Mami keyiwa bintu ji take da ita tamkar er cikinta.
shiyasa suka d'auki qudirin itama sae sun lalata wnn soyayyar dake tsakanin su baza su bar bintu taji dad'i ta koina ba.

Bintu kuwa shiru shiru take ji har dare waheed bai dawo ba tayi kiran wyr sa kmr me bata shiga ganin haka yasa ta kira ummarta taji shin waheed ya taso kuwa?
umma tace waheed kam ae tun qarfe biyar mukayi sallama dashi acewar zae dawo bai iso bane har yanzu.
Komai Bintu bata ce da umma ba sae kashe waya tayi ta soma kuka kaddai wani abu ne ya sami waheed basu da labari.
Umma tayi ta kiranta a waya bata d'aga ba.
Jim kad'an mami ta shigo d'akin ta same ta sae kuka take bata tambaye ta dalili ba sbd yanzu ta gama waya da ummar bintu shiyasa tasan dalilin kukan nata .
Ta zauna taja ta zuwa jikinta sae rarrashin ta take tana kwantar mata da hankali kan inshaa Allah ba abinda ya sami waheed yana nn dawowa lfy.
Kae zancen nata keda wuya kuwa suka ji sallamar waheed ya shigo d'akin idon sa qyar akan bintu wacce tayi saurin d'agowa tana kallon sa da hawaye sha6e sha6e akan fuskar ta.
Cikin damuwa yace"Mami lafiya me Fatima keyima kuka dan Allah kaddai wani abu aka mata"
Mami tace"har ka tambaya bayan tun qarfe biyar aka ce mana ka taso amma har kusan qarfe goma shiru baka ba labarinka kuma wyr ka a kashe bata shiga ae dole hankalin mu ya tashi waheed.
Jiki sanyaye yace"kuyi haquri mami wlh a qarfe biyar d'in nn har na taso junaid ya kirani inzo dan Allah muci liyafar yinin biki da en matan amarya suka shirya mana shine na juya na koma sbd naga a bikin mu ba irin qoqarin da junaid bai mana ba hkn yasa naga bazan iya musa masa ba kan dole na koma,da zan zo ma har nuna min yayi bai ji dad'in da banzo da Fatima ba sae

da na gaya masa uzurin da ya hana muzo tare snn yace ba komai.
Mami tace"to amma waheed ae ba haka ake yi ba ya kamata ace ka kira mu ka snr damu dmn hankalin mu ya kwanta amma sae kaje ma ka kashe wyr ka gabad'aya.
Sosai ya kwantar da muryar sa yace" Am sorry Mami wlh bansan na kashe wyr ba sae yanzu da na fito mota zan shigo na lura,
amma dan Allah mami kuyi haquri kunji".
Ajiyar zuciya Mami ta sauke snn tace "shike nn ae sae ka rarrashi er tawa ni bari in tashi ina zuwa.
Nan ta fita waheed ya zauna gab da bintu had'e da janyo ta zuwa jikinsa yasa hannu sae share mata hawaye yake yana qara rarrashin,a cikin rarrashinta da yake ne ya kama bakinta da nashi ya had'e yana tsotsa cikin nuna kewar ta da yayi ita ma ta biye mishi suna ta tsotsan bakin juna.
Can sukaji alamun mami zata shigo bintu tayi saurin janye jikinta daga nashi.
Mami ta shigo d'auke da abinci da lemu cikin tray,
bintu ta tashi da saurin ta ta kar6a ta ajiye a gaban waheed.
[12/6, 6:27 AM] Billygiro😊: *_🎱BINTUWAHEED🎱_*

*_Story n written by Billy giro😊_*

*_page 9&10_*
Waheed ya kalli trayn abincin da niyar cewa bazai ci ba a qoshe yake,bintu tayi saurin dakatar dashi ta hanyar mintsilar shi ta gefen cinyar sa har sae da ya saki er qara ya kalle ta tayi saurin matsawa d'an nesa dashi bakinta rufe da tafin hannunta tana masa dariya ciki ciki.
Mami tace"lafiyar ka me yake faruwa kana ma 'yata kallon tuhuma haka"
A d'an shagw6e yace"yanzu mami baki ga abinda ta min bane har sae da na saki er qara kuma kinji".
Murmushi kawai Mami tayi ta kalli bintu dan taga lokacin da ta mintsile shi.
Ta maida duban ta gare shi tace"sauqin abin nasan halinka ba yau ka saba ma 'yata sharri ba dan haka yi kaci abinci ku tafi dare nayi".

Daga haka ta bar d'akin ba tare da ta jira taji me zae ce ba.
Kmr jira waheed keyi yaje zae kamo bintu tayi saurin matsawa bata san ta kawo qarshen gefen gado ba sae jin kanta tayi qasa waheed ya fad'o akanta cikin dariya ya kama kunnenta yace"dan Mami na shigar miki shine kika rainani koh"
Ta girgiza kanta cikin dariya mae kmr kuka snn tace"Wash Allah wlh a'a ba hk bane bana son kace ka qoshi bayan mami ta wahala da girka maka abinci"
Waheed ya saki kunnenta a hnkli yana kallonta da kulawa yace"kinji ciwo ne"
Eh qafata
Da saurin sa ya tashi zaune itama ya tada ta yana duba qafar yace"sannu da zafi sosai?
A'a ba zafi na d'an bugu ne kad'an.
yayi shiru sae qara duba qafar yake yana d'an matsa ta a hnkli.
Tayi murmushi tace"kar ka damu ba wani zafi sosai kaci abincin ka kawai mu tafi dare nayi.
Nan ya jayo trayn abinci ya ajiye a gaban su, bintu ta d'ibar masa a plate tuwon semo ne da miyar ku6ewa d'anya sae qamshi ke tashi tasa hannu tana bashi a baki yana ci.
Yace"ke bazaki ci ba?
Tace"um um naci tare da mami"
Komai bai sake cewa ba taci gaba da ciyadda dashi har sae da yace ya ishe shi snn ta bashi lemu da ruwa yasha,yasa tissue ya share bakinsa ya kama lallausan hannunta ya share mata shi tas.
Duk abinda suke mami na tsaye a bakin qofa tana kallon su,
tana mae qara jin son bintu a cikin ranta er qarama da ita amma ta iya bawa miji kulawa.
Sallama ta musu da suka amsa snn ta qaraso daga ciki, bintu ta d'auki tray zata fita dashi zuwa kitchen
Mami tace"Aa kawo d'auki mayafi kuyi ku tafi goma har da mintina ga anguwar taku da d'an jayawa.
Bintu bata bata tray d'in ba tace ta bari kawai takai
Mami bata musa mata ba sbd tasan ko kad'an bintu bata so ta ganta tana wani aiki tace"to jeki kikai amma halinki ne na sani Fatima kin ga damar kice sae kin wanke kwanikan dan Allah kar kiyi hkn ki barsu Hajjo na nn zata wanke kinji,cewa da mai aikin ta.
Bintu tace"to" snn taje ta kai kwanikan bata fito kitchen d'in ba sae da tasa handwash ta qara wanke hannunta.

Da zasu fito Mami ta rako su suka shiga mota suka tafi snn ta koma daga ciki.

Washe gari da asuba waheed ya tashi bintu sae miqa take tayi dan ba kad'an ba waheed ya saukar mata gajiya a daren jiya.
Rumfa ya mata idanunta cikin nashi tana kallon shi cikin shagwa6e fuska tace"uhm yaya agajiye nake wlh kuma bacci bae ishen ba har ji nake kmr kar inje school yau"
Gefen fuskar ta ya shafo da kulawa yace"am sorry muje muyi wanka idan munyi sallah sae ki d'an qara yin bacci koh.
Tace"to yaya break fast fa"
Kar ki damu muje muyi wanka tukun.

Ya qarashe mgnr ne had'e da miqa mata hannu ta kama hannun nasa ta tashi suka tafi bathroom.

A nan inda sukayi sallah ko hijab bata iya cirewa ba tayi pillow da cinyoyin sa ta soma bacci.
Sae da baccinta ya d'anyi nisa ya cire mata hijab snn ya zame jikinsa a hankali yaje ya d'auko mata pillow ya kwantar da ita akai,shi kuma ya tafi kitchen ya soya musu arish da qwai da ruwan zafin tea.

Duk da yana gudun kar suyi letti bai yi saurin tada ita ba har saida ya kwatanci ta d'an sami yin bacci snn ya tashe ta suka shirya byn sunyi break fast suka bar gidan in time ba tare da sunyi letti ba.

Tunda qarshen sati yazo bintu ta soma shirye shiryen zuwa kebbi ta kuma tanadi tsarabar ta mae yawa da zata kai musu sbd wancan karon fushi bai bar ta musu tsarabar komai ba.
Kuma wannan karon tafi yin farin ciki sosai sbd Antin ta Hafsa da Antin ta nafee suma sunce mata a qarshen satin nn zasu je kebbi,rashin jin dad'in ta d'aya yayan ta Abdallah baya nn yana can zariya inda yake karatu.
kuma qarin damuwar ta shine wani babban yayan su mae suna Abbas dake aiki abuja yana nn yazo gida gashi ko kad'an basa shiri ita da dashi sbd rashin jinta komai tayi gwasale ta yake sam baya bari ta shaqata amma tunda aka kusa auren ta ya soma d'an d'aga mata qafa ko tayi wani abun rashin ji sae yayi kmr ma bai ganta ba.

Ranar juma'a da yamma suka tafi kebbi gida ya cika sae murnar zuwan su ake dan kusan lokaci d'aya suka isa dasu Antin ta Hafsa da nafee.
Iyayen su zeenah wato matan sauri ga umma ba murna a tare dasu sae tsegumi suke tayi suna ta maganganun banza da habaice habaice marasa kae dan kawai su samu a tanka su amma ko d'aya basu samu wanda yace dasu uffan ba har bintu kuwa da duk cikin su tafisu fad'a kuma tsaf zata iya ci musu mutunci ba ruwanta da matan qannan mahafin ta ne acewar ta tunda basu d'auki girman su ba itama bazata basu girman su ba.
Ko yanzu dan umma ne kawai yasa taqi tanka su sbd akoyaushe umma sae tace komai zasu ce su sa musu ido kawai kmr ma basuji ba sbd umma mace ce da bata son tashin hankali da anyi ance kuma ba yau ba tasan halin matan saurin nata rigima kawai suke nema ayi ta fad'ace fad'ace sam basa son suga mutum ya zauna lafiya dan har tsakanin su ma idan suka tashi ba ragawa juna suke ba.

Wannan karon mahaifin su yana nn sae murna yake da zuwan su yana ta sa musu albarka kan irin tsarabar da sukayo dan kaf gidan ba wanda basu mae tashi tsaraba ba.

Duk da cewa wnn karon bintu bata had'u da yayanta Abdallah ba sosai taji dad'in kwana biyun da sukayi sbd yayanta Abbas da take shakkun fad'an shi sam bae takurata ba sae ido kawai ya zuba mata tana abubuwanta.

Bayan sun koma sokoto ne rnr Monday da yamma bintu ta fito daga wanka taje gun dressing

mirror ta zauna had'e da yaye towel d'inda ke jikinta ta d'aura tafin hannun ta a hnkli kan nipples d'in ta dake mata masifar ciwo da ta rasa gane dalilin hakan dan tun ba yau ba ta fara ji amma sae ta share bata d'auka ciwon zae ci gaba ba.
Janye hannunta tayi a hankali tana tunanin da kamar tasan cewa ciki yana kawo ciwon qirji.
Ras gabanta ya yanke ya fad'i ba makawa ciki ne da ita dan yau kusan three months knn rabon da taga tayi period gashi zuwan nn da tayi kebbi kowa sae cewa yake ta qara haske da kyau waheed kuma sae gaya mata yake qirjinta yana cikowa wanda tabbas ta fahimci hkn amma sam bata kawo ciki ne da ita ba sae yanzu.
Idan kuwa hakane ya zatayi da cikin nn dmn dae bata shiryi kar6ar sa ba tafiso sae ta qara shekaru dai dai ta kammala karatun ta.
Kwallah ne suka ciko tap a idonta a yanda take da qananun shekarun nn in tabar cikin nn zata iya kamuwa da ciwon yoyon fitsari kmr yanda su zeenah suka gaya mata.
Karar bud'e qofar da taji ne yasa ta maida towel a jikinta ta d'aura tana mai kallon waheed da ya shigo d'akin har ya qaraso kusa da ita yaja stool ya zauna d'auke da damuwar da ta bayyana a fuskar shi ya kama hannuwanta ya riqa yana mae kallon idanuwanta da suke cike tap da qwallah muryar sa a natse yace"me yake faruwa ne my lady?
Girgiza kanta tayi tare da saurin share hawayen da suka gangaro kan kumatun ta, muryar ta can ciki mae cike da jin kuka tace"ba komai".
[12/6, 6:27 AM] Billygiro😊: *_🎱BINTUWAHEED🎱_*

*_Story n written by Billy giro😊_*

*_page 11&12_*
Aa fatima da akwai komai gaya min mene ne.
Ba komai yaya ta fad'i hkne tare da neman alfarmar dan Allah ya barta tana son kasance wa ita kad'ai.
Ba yanda waheed ya iya ya tashi jiki sanyaye ya bar d'akin.
Haka ma Bintu jiki sanyaye ta tashi ta nemi er doguwar riga ta saka snn taje kan bed ta kwanta cike da tunanin mafita.
Tun lokacinda waheed ya fita d'akin bae sake dawowa ba sae guraren qarfe tara na dare da

shigar sa d'akin,
bintu dake kwance cikin shirinta na bacci tayi saurin sa hannu ta share hawayen fuskar ta.
Waheed yazo kusa da ita ya zauna a natse sae kallonta yake har ta tashi zaune snn yace"fatima gaya min me kike ma kuka"
Kanta qasa ta girgiza kanta a hnkli murya can ciki tace"ba komai"
Shiru waheed yayi yana kallon ta ya shiga tunanin shi kuwa me yake damun fatima da bata son gaya mishi.
Can yace"to tashi muje muci abinci"
Tace"um um na qoshi"
Me kika ci da har kika qoshi?
Ba komai amma na qoshi.
Aa hkn ba zae yiyu ba fatima tashi muje muci abinci kuma kar kimin gaddama.
Sosai taji ya takura ta dmn sam bata jin cin abinci damuwar da take ciki kad'ai ta ishe ta,amma ba yanda ta iya dole ta tashi suka tafi amma duk da haka ta kasa cin wani abincin kirki sae waheed ne yaci koshi ba sosai ba.

Daren yau sae ya zamo ma waheed ba dad'i sbd yanda bintu taje can nesa dashi ta kame guri d'aya cikin damuwar da take d'auke da ita amma kuma tausayin waheed na ranta dan tasan dole bazai ji dad'in yanayin da take ciki ba gashi kuma ya saba kullum idan baya sameta ba sam baya jin dad'i amma ya ta iya,
tana jinsa ko bacci ma ya kasa yi sae juyi yake tayi da qarshe ya tashi ya tafi bathroom ya d'auro arwala ya shiga yin nafilfli.

Washe gari haka ta tashi ba wani qwari a tare da ita komai a sanyaye take yin shi har suka bar gidan.
waheed ya ajiye ta school snn ya nufi gurin aikin shi cike da tunanin me ke damun fatimar shi da bata son snr dashi,
bcos ko da safen nn ma sae da ya tambaye ta tace mishi ba komai.

Bayan sun gama lectures ne suna zaune a bakin classes ita da su zeenah sun sata a gaba sae tambayar ta suke abinda ke damunta ko sunyi fad'a ne ita da waheed.
Tace"in fad'a ne da sauki akan abinda nake ciki"
Zeenah tace"Ayya mene ne kike ciki gaya mana idan wanda zamu baki shawara ne sae mu baki shawara.
Sae da bintu ta fitar da numfashi a hnkli snn tace"ina d'auke da ciki kuma bana son kowa yasan dashi sbd ban shiryi kar6ar sa ba"
Kallon juna sukayi sarah tace"meyasa baki shiryi kar6ar sa ba?
Sanin kanku ne a iya shekaruna banko isa ace na kammala secondary school ba dan anyi sakko sani makaranta ne yasa nayi saurin kammala ta amma har yanzu still en tsarana na can basu kammala ba.
Shiyasa nace muku ban shiryi kar6ar cikin nn ba sbd qananun shekaruna nafi son sae nn gaba tukun.
Zeenah ta nisa snn tace"ae kam dama nasan haka zata faru, ciki ba.....um um kar ki soma

zeenah ni shawarar ku nake so ba wasu qananun maganganu ba.
Zeenah tace "har wata shawara ce kawai ki zubar da cikin mana"
Da sauri sarah ta kalli zeenah bintu kuwa tayi saurin girgiza kanta tace"Aa ni bazan iya ba ina tsoro"
Zeenah tace"au daa a tunanin ki me zakiyi idan baki zubar ba byn da kanki kince baki shiryi kar6ar cikin ba"
Nima ban sani ba zeenah kuma ina tsoron zubarwa amma ko kad'an wlh bana son cikin nn.
Hm tsoron me to kece farau ko ko akanki aka fara.
Ni ba haka ba ina tsoron kar in zubar wata matsala ta biyo baya.
Kawai kisa a ranki ba abinda zae faru.
To idan yaya waheed yaji fa?
A ina zaiji bayan kince ba wanda yasan da cikin sae mu kad'ai da kika gaya ma yanzu,kuma sanin kanki ne indai mune maganar nn baza ta ta6a fita ba.
Haka ne na yarda daku amma duk da haka ina tsoro da kmr bazan iya ba.
Zeenah tace"to tunda kina tsoro ae sae ki bar cikin amma ina ji maki tsoron kamuwa da ciwon yoyon fitsari sbd sanin kanki ne kinyi qanqanta da haifuwa kuma da idonki a nn asibitin kinga masu fama da irin wnn lalurar mafi yawan su duk qananun yara ne irinki da akayiwa auren wuri.
Bintu tace"nima abinda nafi jin tsoron sa knn kuma ko ba komai nafi son sae na kammala karatuna tukun dmn bana jin lokaci d'aya zan iya lalurar renon yaro da kuma karatu.
Nima shi nake jiye maki amma kije kiyi shawara tukun.
Tace"shikenan zanyi shawara"
nn ta tashi had'e da fad'in ni zan tafi gida a qafa nake son in taka yau.
Nan sukayi sallama da juna ta wuce.
Rae 6ace sarah ta kalli zeenah tace"haba dan Allah zeenah kan me zaki bata shawarar ta zubar da ciki,ae da kin barta dashi in yaso karatun ta ya ta6ar6are kowa ma ya huta.
Hm sarah ke karatun ta ya dama ni burina in lalata rayuwar ta gabad'aya ta kasance ba inda zata saka kanta taji sanyi,dan haka ki zuba min ido kawai idan bazaki iya ba danke na fahimci qaramar qwaqwalwa ce dake.
Shiru kawai sarah tayi bata ce komai ba.
Bintu kuwa tana isa gida shigar ta keda wuya waheed ya kirata a waya yana tambayar ta meyasa taje gida a qafa bata kirashi ya turo mata driver ba.
Tace"yaya ba komai haka kawai naji ina son in taka a qafa"
No Fatima bana so kar ki sake dmn na tabbatar kafin ki isa gida kin sami wani ya tare ki a hanya.
Shiru tayi sbd hkne d'in wani ya tare ta a hanya sae dai bata kula shi ba ta wuce,haka take fama kusan duk lokacinda ta fito ita kad'ai sae wani ya tare ta a hanya yace yana sonta shiyasa sam waheed baya son fitar ta ita kad'ai,rnr ma tare suka fita amma sae da wani ya tare su a hanya yace da waheed dan Allah ina son er qanwar nn taka kuma wlh da aure nake sonta,sosai waheed yaji kishi a ransa amma hkn ya jure ya masa bayanin cewa matar sa ce ba qanwar sa ba, haquri mutumen ya bashi waheed bai kula shi ba yaja bintu suka bar gurin.
Waheed ya katse ta da shirun da tayi yace"fatima kimmin shiru wani ya tare ki a hanya knn koh?
Bata ce mishi eh ba sbd bata son ranshi ya 6aci sae ce masa tayi yayi haquri.

Yace"ae baki min laifi ba Fatima kawai dai ina so ki kiyaye kinji"
Tace"inshaa Allah zan kiyaye"
Daga haka suka tsinke wayar bintu ta rage kayan jikinta,ta zamo daga ita sae vest da d'an guntun wando tsayin sa iya cinya.
taje kitchen ta d'aura musu abinci bayan ta gama taje tayi wanka ta shirya abinta cikin qananun kaya sae zuba qamshi take amma kallo d'aya zaka mata kasan cewa tana cikin damuwa da tunani sbd tun lokacinda ta baro school cike take da tunanin shawarar da zeenah ta bata.

Koda waheed ya dawo gidan ya same ta zaune a falo tayi shiru ga Tv na aiki amma hankalinta baya gurin.
Kusa da ita yaje ya zauna,
a sanyaye bintu ta d'ago ta kalle shi had'e da yi mishi sannu da zuwa.
Shima jikin nasa a sanyaye ya amsa dan dae ba haka ta saba yi mishi sannu da zuwa ba,da murnar ta take zuwa ta rungume shi cikin so da qauna ta mishi sannu da zuwa.
Numfashi ya fitar a hnkli snn ya tafi da ita zuwa cikin sa muryar sa a natse cikin kulawa Yace"Fatima dan Allah gaya min meke damunki kinji.
Kae tsaye taji qwalla sun cika mata ido sbd tambayar ta da yake yana qara saka ta a cikin damuwa gashi kuma bata iya snr dashi cewa ciki ne da ita kuma bata shiryi kar6ar sa ba.
Waheed dake kallon ta yasa hannu ya share mata hawayen da suka silalo kan fuskar ta.
Snn yace"tashi muje d'aki inji mene ne"
Bata musa masa ba yaja hannunta suka tafi d'akin shi cikin lallami da rarrashi yake tambayar ta amma bai gane komai ba sae ma kuka ta ajiye mishi kan dole yabarta.

Haka ta kwashe sati d'aya kullum cikin tunani da damuwa ta kasa yarda da shawarar zeenah dmn tana tsoron kar wata matsala ta biyo baya amma sam bata son zaman cikin,
gashi bata san wa zata kira ta sanar matsalar da take ciki ba a cikin antin ta Hafsa ko Nafee dan tasan fad'a zata sha na qwarai har sae ta gwammaci bata fad'a ba d'in dan har umma zasu iya snr ma idan kuwa umma taji kashin ta ya bushe.
Ga ciwon qirjin nn sae damunta yake wani lokaci da qyar ma take samu a gama lectures ta dawo gida.

Da yake yau weekend ne suna zaune a d'aki suna fira ita da Antin ta Hafsa waheed bai san da zuwanta ba sae da ya shigo d'akin ai kuwa da murnar sa suka gaisa yace"wlh dama ina son ganin ki hafsa tun washe garin rnr da muka dawo garin nn gabad'aya na rasa gane kan Fatima kuka take yi in na tambaye ta tace min ba komai duk satin nn haka ya qare min cikin damuwa ba yanda banyi da ita ba ta fad'a min in nayi mata wani laifin ne sae in bata haquri amma taqi ta gaya min wai ita ba komai.
Anti Hafsa ta kalli bintu wacce tun lokacinda waheed ya fara zancen sa ta sadda kanta qasa.
Tace"hm"kafin take maida dubanta ga waheed tace"kasan ina shigowa gidan nn kallo d'aya na mata na gano cewa tana cikin damuwa kuma duk tabi ta rame amma dana tambaye ta cemin tayi ba komai dan ta tashi daga bacci ne, duk da ban ganmsu da abinda tace min ba amma sae ban matsa mata ba sbd ban sani ba ko wata matsala ce a tsakanin ku da bata son kowa ya sani shine kawai yasa na basar muka ci gaba da fira, a niyar in zan tafi in bata shawara kan koma

mene ne ta riqa haquri ta daina saka damuwa da yawa a ranta haka, sae gashi ashe kai d'in ma baka san meke damunta ba.
Wlh kuwa Hafsa kuma in nace in matsa tambayar ta kuka take ajiye min snn abincin kirki ma ta daina ci kuma ta daina bacci a d'akina shine nace inaga dae ni na mata laifi ban sani ba.
Bintu ta girgiza kanta cikin muryar kuka tace"wlh yaya ni baka min laifin komai ba"
Yace"to meyasa kika qauracewa d'akina kika daina bani duk wata kulawa da kike min amma tun da kin rantse kince ban miki laifi ba kuma baza ki iya gaya min abinda ke damun ki ba ina son dan Allah ki snr da Hafsa damuwar ki dmn ta baki shawara a sami mafita in samu in daina ganin ki a cikin damuwar nn fatima wlh bana jin dad'i ko kad'an kuma kin sani. Bintu tace"yaya na gaya maka ba komai"
Rai 6ace Anti Hafsa tace"wlh zan mareki in kika sake fad'ar ba komai d'in nn very stupid kin maida mu qananun yara ne da bama gane damuwa ko me!
Kuka bintu ta fashe dashi
Waheed yace"Aa Hafsa dan Allah ki mata a hankali.....wane irin na mata a hankali bayan kace ba irin lallashin ta da baka yi ba amma taqi gaya maka.
Kiyi haquri dae dan Allah ki lallashe ta har ki samu ta gaya miki ni bari in fita.
Bai jira amsar ta ba ya fita.
A natse anti Hafsa tace"haba bintu kince ba komai kuma kince waheed bai miki laifin komai ba to me kike so kice damu ki dubi yanda bawan Allah nn duk yabi ya rame lokaci d'aya sbd damuwar da kika saka kanku a ciki shin ba kya jin tausayin sa ne idan ya miki wani laifin ne a rashin sani ki gaya masa mana sae ku sulhunta kanku.
Bintu tace"wlh Anti bai min laifin komai ba"
To gaya min me yake damun ki kuma kar kice min ba komai.
Damuwa ta d'aya ce Anti test6 d'in da mukayi last week shine naji ance da dama ba'a ci wani abin qwarai ba shine duk nabi na damu kar in kasance cikin wa enda basuci abin qawarai ba.
Ajiyar zuciya Anti Hafsa ta sauke tace lallai bintu son karatun nn naki yana neman zautar dake hm kai ni ban ma yarda da zancen nn naki ba har kece zaki saka damuwa har da su kuka akan jin tsoron fad'uwar test keda sam ba kya wasa da karatu bare kiyi tunanin fad'uwa.
A d'an daburce tace"Anti ni gaskiya na gaya miki kuma komai dagewa ta akan karatu ae sae Allah ya cishe ni snn ko zanci".
Au kin san da haka shine baki roqi Allah ya cishe ki d'in ba zaki wani saka damuwa a ranki har dasu kuka,ni ban yarda ba gaya min gaskiyar abinda ke damunki ko kuma wlh in snr da umma.
Ganin antin ta na son gano ta tashi cike da kukan shagwa6a tana fad'in"haba Anti Hafsa gaskiya ni ki daina min haka ae kinsan bazan miki qarya ba ko umma kika kira wlh abinda zan iya gaya mata knn uhm uhm....ta bar d'akin cikin kuka ta nufi falo,
waheed dake zaune a falo ya taso cikin sauri ya qaraso gurinta ta fad'a jikinsa tana ci gaba da kuka.
Kafin yace komai sae ga anti Hafsa ta fito cikin damuwa yace"haba Hafsa keda nace ki mata a hankali shine zaki sake saka ta kuka Allah dai yasa ba dukan ta kikayi ba"
Murmushi Anti Hafsa tayi tace"ae kasan halin bintu ni ba abinda na mata daga kawai ta gaya min damuwar ta nace ban yarda ba shine fa, kaji kaji kaji ta gaya masa duk yanda sukayi da bintu.
waheed yace"to Hafsa ae kinsan karatun secondary school da wnn ba d'aya bane, wnn yafi

wuya nesa kinga dole ta d'an saka damuwa a ranta har dai yanda akace mutane da dama basu ci ba.
Anti Hafsa tayi murmushi tare da fad'in to ae shikenan na yarda sae ki daina kukan.
A hnkli waheed ya shafo gadon bayanta d'auke da murmushi a fuskar sa bakin sa saitin kunnen ta yace"kinji anti Hafsa tace ta yarda daina kuka hk kar kisa baby na yayi baqin rai.
Da sauri ta d'ago cikin fargaba tace "wane babyn"
Hancin ta ya lakato snn yace"babyn ina fata mana"
Dukan shagwa6a ta kai masa a qirji snn ta rungume shi tana sauke ajiyar zuciya a hankali.
[12/6, 6:27 AM] Billygiro😊: *_🎱BINTUWAHEED🎱_*

*_Story n written by Billy giro😊_*

*_page 13,14,&15_*
Saurin d'agowa tayi daga kan qirjinsa sbd tuna cewa Antin ta Hafsa na tsaye a gurin sae dai koda ta duba bata ganta ba ashe ta tafi d'aki tace"yaya bari inje inga anti Hafsa tace min ba jimawa zatayi ba akwai inda take son taje.
Ya gyad'a mata kae ta tafi ya hard'e hannuwan sa a qirji sae kallon ta yake har ta shige d'aki snn yayi murmushi had'e da girgiza kansa yace"fatima iyayen rigima Allah ya nuna min kin haifa min baby inga ya renon zae kasance er zan kama ko mamar.

Koda bintu ta isa d'aki ta samu har anti Hafsa ta d'auko jakarta zata fito bintu ta 6ata rae tace"haba Anti ba dai har zaki tafi ba"
Tace"Bintu kinsan na gaya miki sauri nake ba jimawa zanyi ba na biyo ne kawai in ganki"
To anti me zaki ban kafin ki tafi?
Er dariya tayi tace"kmr ya me zan baki"
Anti ina wani turaren da kika ta6a bani mae dad'in gaske d'in nn ya qare min kuma wlh ina son shi ya za'ayi?
Yako za'ayi qwara d'aya kacal nake da shi yanzu hk,ta ciro shi a cikin jaka tace kin ganshi kuma shine nake aiki dashi ba kuwa zan baki ba sae dai in nemo maki.
A shagwa6e tace "Plz anti ki bani shi sae ki samar ma kanki wani"
Tace"Aa kedai zaki haqura har in samar maki dan gskiya bana son wnn turaren ya katse min.

Uhm haba dae Anti dan Allah
Hm ni kinga tafiya ta nasan da kin fara rigimar nn taki 6ata min lokaci kawai zakiyi a banza.
Daga haka taje zuwa fita har ta bud'e ganbu bintu tayi saurin riqo hannunta tace"to tsaya kiji mana anti"
Fad'i ina jinki.
Kmr yaushe za'a sami turaren?
Ko gobe ma za'a iya samun shi dan d'azu ta kirani take ce min ta d'auko kaya.
Hln nawa take saida turaren ne to?
5k ne amma bari zan saya miki.
Nifa Anti har biyu nake so.
To inji dumus dan dae wlh bazan iya cire 10k wa ke kad'ai ba bayan nima ina son in siya.
Er dariya bintu tayi tace"kae Anti nifa er qanwar kice ko goma nace ae zaki iya keda duk wata yaya yusuf albashi yake maki.
Da wasa ta harareta tace"Aa ba albashi yake min ba mae yin albashin yake kawo min gabad'aya"
Bintu ta fashe da dariya tace"to muje gun yaya waheed in ce ya bani"
Kae bintu yanzu har sae kin tambaye shi bayan duk irin kud'in da yake baki"
Wlh yanzu ba kud'i a hannu na ne Anti ae da bazan tambaye shi ba kuma baki ga yanda yake matuqar son qamshin turaren nn ba wlh shiyasa nake so in siya har biyu suna d'an jima min kafin su qare.
To shike nn muje ki kar6a.
